Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.17 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Wawa Mugunyar Tsirfa, Uba na Fada Uwa Na Kuka: Lalaben Tarihin Karabkiya Tsakanin 'Yan Tauri a Bakin Makaɗa Kassu Zurmi. Bitar Wasu Daga Cikin Waƙoƙinsa

**Ibrahim Muhammad**
Danmadamin Birnin Magaji
Inkiya Fadar Mai Martaba Ɗan'alin Birnin Magaji,
Birnin Magaji Jihar Zamfara,
Jihar Zamfara Nijeriya

**Corresponding Author: Ibrahim Muhammad** birninbagaji4040@gmail.com
+2348149388452

## Tsakure

Kassu fitacce ne a waƙoƙin, noma, farauta, tauri da ɗan'hali. Shi ya sa aka kira shi makaɗin Maza. Ba a kalli Maza a matsayin jinsi ba a nan, sai dai masu ƙarhin hali wajen murza wasu ayyuka masu wuya ta fuskar gwarzontaka. Wanda ko ya koma daji ya tare a muhalli ɗaya da miyagun ƙwari da namun daji waɗanda Allah ya keɓe su a dajin, da wanda ya wulaƙanta darensa da ranarsa domin ya firgita wanda ya samu halaliyarsa a tsakiyar daren da rana ya kwace masa ƙotonsa, wato mai ɗan hali, in aka haɗa da wanda kullum tunaninsa bai fi nuna buwaya ba a bayyane da ɓoye ba, wato Dantauri, to waɗannan su ne Kassu ya shahara wajen yi ma waƙa. Na daɗe ina tattara waƙoƙin Kassu. Na mayyeze ƙumshiyarsu kamar yadda nissan Kassun shi kansa. Na sha binsa ina neman tafsirin fasaharsa tun ina Dankachaurana. Na ga lokaci ya yi da zan ɓarge gumina domin tabbatar ma ɗalibai 'yan uwana cewa Kassu fasihi ne ta fuskar adana tarihin waɗanda suka yi sunan su maza ne musamman a cikin al'ummarsa. Wannan tsakure zai taƙaita kansa ne a nazarin wata karabkiyar da ta wanzu tsawon zamunna tsakanin 'yan Tauri na yankin da shi mawaƙin ya yi nasa zamani. Sai mun haɗu a cikin zubin wannan maƙala domin ku sha labari.

**Keɓaɓɓun Kalmomi:** Wawa Mugunyar Tsirfa, Uba na Fada Uwa na Kuka: Lalaben Tarihin Karabkiya Tsakanin 'Yan Tauri a Bakin Makaɗa Kassu Zurmi. Bitar Wasu Daga Cikin Waƙoƙinsa

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Waƙar baka kam sam barka a wannan zamani, domin tsohhin hannu da masu biɗat hannunsu su daidaita wajen rattaba abinda suka kalato sun yi namijin aiki kuma sun duɓufa suna nan suna yi kan sai sun katibe duk wani mai fasahar baka a cikin al'ummarsu. Wannan shi zai hana tarihi ya ɓace. Babu ko yadda za a martaba al'ummar da ba ta da tarihi. Shi ko tarihi sahihancinsa sai da fasahar baka. A cikin nau'u'ukan fasaha ta baka, babu kamar waƙar baka. Ita kuma waƙar baka ta zama tamkar wani rumbu na adana tarihin masu fasihancinta, kuma da ita ake aika saƙonni, da kuma tanadin tarbiyyar al'umma.

Ba a gama yayin waƙa, balle ta shuɗe. Haka nan, ana samar da waƙoƙi ga duk wani al'amari da ya taso domin faɗakarwa da adana tarihi. Da haka nan mawaƙa suka adana mana tarihin kowane al'amari na rayuwar da ta shuɗe, Da ba don hkan ba, da ba mu san tarihin gidaje da unguwanni da garuwa ar ma da manyan ƙasashemmu ba. Kassu Zurmi a shahararsa ta waƙar baka, ta say au an yi g*angami irin na hawan sallar idi* domin a tana da shi, a karrama sunansa da rayuwarsa da iliminsa da wafatinsa. Waƙoƙin da ya yi sun zama rumbun adana tarihin ƙasar Hausa in anka nazarce su da kyau.

Za a taɓo tarihin Kassu, da nau'o'in waƙoƙin da ya yi wa wasu rukunnan jama'a kamar manoma, mafarauta, maɓannata, da masu ji da bajinta. Da wannan garambawul nake bayyana cewa "wawa mugunyar tsirfa" na nufin wasoson da 'yan farauta da 'yan tauri ke yi a jeji wani yanayi ne mai haɗarin gaske ga rayuwa, amma a wurin waɗannan bayin Allah, gwada sa'ar bajinta ne, kuma sun yanke ƙauna ga rayuwa ko a mutu ko a yi rai.

## 2.0 Gadon Gida a Lale ga Raggo: Kassu Jarumci Gado Kayyo[1]

Zaman Kassu ba makaɗin 'yan zamani ba, amma sai lokacin wannan yunƙuri na karrama shi aka fahimci duniyar makaɗa da ɗalibai da masu nazarin tsofaffin waƙoƙin baka, bas u manta da Kassu ba. Dalilai birjit ne dalilin fahimtar haka. Misali idan aka nemi asalin mahaifar Kassu domin tantance tushensa, sai a fahimci shi ba Bazamfare ba ne ga asalinsa. Kassu ya ayyana cewar shi Bagobiri ne daga Kurawa ta Sabon Birnin Gobir a shaidawarsa

Rad da Allah yay yoni,
Kassu rad da maisama yay yoni,
Ka ganan nan ban zo kiɗi ba Sabon Birni,
Sai da Ummaru yay kiranmu Sabon Birni,
Sanda jikan Shawai,
Ummaru jikan Shawai: zuriyag gidan Jari Kada.

**Jagora:**
Sai da Ummaru yay kiranmu Sarki niz zo,
Amma in bancin rashin sani,
Ba baƙo ba ne gid nid dawo: gida Kurawa,
Don hwaɗa aka tsoron zuwa gidan Jangwarzo.

[1] . Wannan karin magana ta ginu ne bisa wani ilmi da al'ada wanda kuma addinin musulunci ya tabbatar da shi shi ne, koda mutum raggo ne a yanayinsa, to ba zai rasa yin gadon gidansu ba.

A tattaunawar da aka yi da Kassu, kakansa Gandau Sarkin Fawa shi ne dalilin tasowarsu daga Kurawa suka zauna a garin Dunfawa ta yanzu aka haifi uban Kassu Malma Muhammadu Ganga shi ya sa Kassu ya taso a garin Kadawa ta yanzu.

**Kirarin Gobirawa**
*Gobir Uwar Faɗa*
*Gobir ta Ɗanhalima kowa Sarki*
*Gobirawa na Bawa kanun yaƙi*
*Gobirawa a ba ku ramcen ƙwaya, ku mai da soshiya don gayya*

Daga irin abinda kunne ya sha ji game da Gobirawa a cikin kirarinsu, sai a fahimci Bagobiri komai tsawon lokaci yana da siffar da kirarinsa ya shaidar game da shi ko a kansa, saboda halayya. Ba a ce ba za a samu ba in an tsawaita bincike, amma akwai alamar Kassu Zurmi yana da jinin Gobirawa saboda bayan ya yi zama makaɗin Manoma wanda sai jajirtacc ke tsayawa ya zama manomi, sai Kassa ya riƙa bin Mafarauta a Daji yana Kuranta su, bayan ya daɗe da nazartar Mazaje masu Ɗanhali wanda su ma ya ci gaba da bayyana halayyarsu a waƙe, su 'Yan Tauris u ne Kassu ya wataya a cikinsu, tamkar shi kansa Ɗantaurin ne. In babu jinin Gobirawa a cikin jiki da tunanin Kassu, ba zai yi sha'awar Gwarzontaka da halin mazaizai ba, balle ya haɗa waɗannan mazaizan ya waƙe su kaf. In ji Hausawa, kamar Kumbo kamar kayan Kumbon. Kassu dai Bagobiri ne, koda kuwa ya taso a ƙasar Zamfara. Lalabe a kan tushen Kassu ya walwale a bakin Kassun shi kanshi don an ga abinda yah hwaɗi da cewa gayyatar da aka yi masa Sabon Birnin Gobir, shi fa ba baƙo na gida yak koma.

### 2.1 Shekarun Kassu Nawa?

Bayan sanin tushen Kassu ai sai a san shekarunsa nawa a duniya kafin ya yi wafati? An haifi Abubakar Kassu Zurmi a shekarun 1910, ya rasu a shekarar 1983 yana da shekaru saba'in da Uku (73) a duniya[2] Kassu ya yi aure yana da shekaru 20 sunan matarsa ta farko Ba'u. Bayan Ba'u ya auri mata uku akwai Gwamma da Inno da"Yaɗɗiya. Kassu yana da jimlar 'Ya'ya shabiyu akwa Aliyu da Namakka da Rabi'u da Aliyu. Kassu ba shi kaɗai yake a wajen mahaifansa ba. Mahaifinsa mai suna Mamman Ganga da Mahaifiyarsa mai suna Mamuna sun haifi 'Ya'ya Uku daga cikinsu Kassu shi ne na farko.

Dalilin Samun Laƙabin Kassu da Zurmi

Kassu dai laƙabi ne da aka saka wa Abubukar Kassu daga gida a dalilin an haife shi ranar Lahadi, wato ranar kasuwar garin Dauran da ke cikin masarautar Zurmi

Zurmi kuma sunan gari ne, amma a maimakon a kira shi da Abubakar Kadawa inda nan ne mazaunarsa, kuma har yanzu a nan ne gidansa da ya bari iyalansa suke zama a halin yanzu, wannan ya samu a dalilin Zurmi it ace hedikwatar gundumar da ke kula da ƙauyen Kadawa a sarauce.

Kassu yana noma da kiwo a matsayin hanyar tafiyar da rayuwarsa da ta iyalansa. Sannan ya ɗauki kiɗa a matsayin hanya ta ilmantarwa da faɗakarwa da wayar da kan jama'a kan abinda ke wakana a cikin al'ummarsa. Kassu bai ɗauki kiɗa a matsayin roƙo ba, domin rukunin waɗanda yake yi ma kiɗan bajinta ce gabansu ba tara dukiya ba,

---

[2] . Malam Aliyu ɗan Kassu na cikinsa ya shaidarda hakan a tattaunawarmu ta baya-bayan nan a ranar 15/04/2020., a gidan sayar da motoci na Gwamnati motors, na garin Gusau, inda muka yi wannan Tattaunawar

kullum suna cikin daji suna neman tsirrai da dabbobi domin su tasirantu da su wajen nuna bajinta da waibuwa.

### 2.2 Matsayin Kassu a Lissafin Wasu Mawaƙan Baka

Ba je nesa kalar batutuwa kan Kassu Zurmi ba, sai aka yi wa kai Turke da wani shahararre a fannin waƙar baka kuma mai waƙar shi ma makaɗin Maza ne, inda ya kawo wani hoto na Kassu Zurmi a cikin fasaharsa ta baka. Misali a cikin waƙar wani shahararren Barawo mai suna Nazaƙi, wanda turken waƙar shi ne Nazaƙi baƙin Barawo na Sakkwato

**(i) Jagora:**
Nicce Nazaƙi wallai kiyay yanni,
Nina ba Ɗanmatti na ba,
Ba Kassu mai waƙakku na ba.
**Gindin Waƙa:** Nazaƙi baƙin bawa na Sakkwato.
A nan Gambu ya tabbatar da Kassu mawaƙin Barayi ne. Shi kuma Kassun ga abinda ya ambata ga kansa:

**(ii) Jagora:**
Kassu na tcere ma Maroƙa,
Kowana ne na kandami kainai,
Na tcere ma Maroƙi.
**Jagora:**
Zani hwaɗa maku abinda nit tcere ma Maroƙa.
**Jagora:**
Kowa nat tahi roƙo,
Sai ya tambaya ga mai samu shi ka jiɗa,
Ni kau in na zo ga wanda ba samun nika shiɗa.
**Jagora:**
Mutun abinai ba ya gudu nai,
Na dai gode ma matcata.

(III) **Jagora:**

Kasan ɓace ɓace ai ba tauri ne ba,
Ni Mamman Kiɗi da waƙa su nig gada,
Alhaji dum mai hwaɗa dani bai san kunya,
Dum mai tauri ƙasag ga munas san tushenai.

**Y/Amshi:**
Don haka dum mai zuwa hwarauta ya san Nomau,
Kuma dum mai Kiɗi da waƙa ƙasagga ya san Kassu.

Gindin Waƙa: **Waƙar Noma ta Ɗangaladima Wada Marakkai wadda Makaɗa Mamman Na Ta'ukka Gandasamu ya yi masa.**
Mamman Na'taukka ne ya gwarzanta Nomau Mafarauci da Kassu a cikin waɗannan ɗiayan waƙa.

Saboda Kassu buƙatarshi ya san halayya da dubarun / wayon waɗanda yake yi ma waƙa, to ba ya buƙatar ya samu wani abu ga hannunsu. Idan bai zo ma mutum da sigar roƙo ba, sai a saki jiki da shi kamar ɗan gida ba baƙo ba, ba kuma maroƙi ba. Daga nan ma ana iya gano halayya da matsayin Kassu.

Wannan tunani na Kassu ya bambanta shi da sauran makaɗa wanda da wuya ka samu makaɗi wanda ba ya son a ba shi wani tallafi sai Kassu

## 3.0 Fasahar Kassu A Waƙe

Kassu waƙoƙin noma ya fara yi, duk da cewa babu gidan rediyo ko Talabijin da suka naɗe waƙoƙin amma shi kansa ya shaidarda waƙar noma ya fara yi kamar haka:

### 3.1 Waƙar Kwazo Dan Sani

Wannan waƙa ce da Kassu ya rera ma wani manomi da ake kira Kwazo, a lokacin amshi ake yi mishi, kuma da ganga ya yi waƙar[3]. An gabatar da wannan waƙa a shekarun 1930 kimanin shekaru taamanin da suka shuɗe. A lokacin Kassu yana matashinsa. Wannan waƙar yi ta a garin Magarya domin mutumin magarya ne aka yi ma waƙar. A duba shafin Rataye domin samun matanin wannan waƙar domin nazari.

### 3.2 Waƙoƙin Kassu a Kan Farauta da Mafarauta

Waƙoƙin Kassu na farauta suna da yawa, ba a samu wanda ya taskace ya ambata adadinsu ba har zuwa wannan lokaci. Daga cikinsu akwai:

i. Waƙar Ibrahim Maishibra
ii. Waƙar Garu-garu
iii. Waƙar Katakare
iv. Waƙar Ibrahim Twasshi Birnin Magaji
v. Waƙar Kaho Kuryar Dambo

### 3.3 Waƙoƙin Kassu a Kan Sata da Barayi

Ko Gambu mai waƙar Barayi ya san da zaman Kassu domin bayanammu da suka gabata sun kawo yadda Gambun ya ambata cewa Kassu sanannn mawaƙin Barayi ne, Daga cikin misalan waƙoƙin Kassu na Barayi ga kaɗan domin masu nazari

i. Waƙar Garba Kura Mai Aciwawi
ii. Waƙar Garba Dunhwawa
iii. Waƙar Sale Gidan Goga
iv. Waƙar Dudu
v. Waƙar Adamu Dodo

Waɗannan waƙoƙi za a samu wasu a shafin Rataye domin ci gaba da nazarin fasahar Kassu a cikin waƙoƙin baka.

### 3.4 Waƙoƙin Kassu Kan Tauri da 'Yan Tauri

Waƙoƙin Tauri a fahimtar mai wannan nazari sun fi Tamanin bisa ga tsawon lokacin da aka ɗauka ana nazari kan mawaƙan baka musamman shi Kassun, am fahimci waƙoƙinsa na Tauri da 'Yan Tauri sun fi yawa. Ga kaɗan daga cikinsu

[3] . Hirar da aka yi da Kassun 3/3/1975

i. Waƙar Labbo na Amadu
ii. Waƙar Audu Nomau Na Magarya
iii. Waƙar Ibarahim Shayi Ɗan Gidan Labbo
iv. Waƙar Korau Kadamutsa
v. Waƙar Basare Shanawa
vi. Waƙar Maidabo na Gidan Duwa
vii. Waƙar Mai Babarbara Shehu Buraguji Birnin Magaji
viii. Waƙar Mamman Alabai Birnin Magaji
ix. Waƙar Aikau Birnin Magaji
x. Waƙar Baƙo na Ɗanƙaya Ɗantsauni

A shafin Rataye za samu wasu daga cikin matanin waɗannan waƙoƙI omin nazari kan waƙoƙin Tauri na Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi.

## 4.0 Wawa Mugunyar Tsirfa, Uba na Faɗa Uwa na Kuka

Wasan Tauri ko Dambe da Kokawa ko Farauta a daji sai namijin gaske, wanda ya shirya tunaninsa da jiknsa a kan hakan, shi ne namiji a wajen al'umma. A ƙarƙashin wannan take na Wawa mugunyar Tcirhwa, ranar da zaka hwara ta uba hwaɗa uwa na kuka yana da muhimmanci ga tauri da 'yan tauri, domin ya bayyana rayuwa da tunanin 'yan taurin. A cikin waƙar ta Ibrahim mai shibra wanda ke nuna cewa duk da amfanin da Tauri ke da shi wajen tsaron al'umma a lokuttan ko ta kwana, amma akwai wasu manyan miyagun ɗabi'o'in da ke tattare ga al'adar Tauri waɗanda ke sa iyaye kuka na bayyane da na zucci kan wanda ya rungumi wannan al'ada da wasannin tauri. Cikin wannan waƙar ne ma aka cirato taken wannan maƙala, aka kuma ƙaraba gaba da taken zuwa ga wannan hamshaƙin taro na ƙasa da ƙasa a kan Kassu Zurmi domin a isar da saƙon shi Kassun ga al'umma kan abinda tauri ya ƙunsa. Ɗan waƙa daga cikin wannan waƙa ta Ibrahim Maishbra ya bayyana da "*wawa mugun tcirhwa, ranar da zaka hwara, uba hwaɗa, uwa na kuka*" A koma shafin rataye a ga cikin wannan waƙa.

## 4.1 Waƙar Labbo na Amadu

Ita wannan waƙar ta naɗe abubuwa kamar haka:

i. Garuruwan da suke a cikin duniyar Makaɗa Kassu misali Jabanda, Barkeji da Baican Dauran, Dauran, Rukudawa da Kaurar Dawa waɗannan duk mazaunar shaharrin 'Yan Tauri ne na duniyar Kassu
ii. Tarihin wanzuwar wasu abubuwa da suka shahi garin Jabanda domin a cikin waƙar ne Kassu ya ambaci rukunin 'yan Tauri kamar akwai rukunin 'Yan Jabanda, da rukunin 'yan Brnin Magaji da 'yan Hwadama da Jangerawa da Barkezawa da 'Yan Rukudawa
iii. Hwaɗace-hwaɗacen da suka bar tarihi tsakanin 'yan tauri na waɗannan rukunnan da aka ambata a sama (ii)

## 4.2 Ɗiyan waƙar Labbo na Amadu[4]

**Jagora:** Gagarau na Mahamman

To,
Na Amadu Labbo mahaukata na Magaji

[4] . Wannan waƙar tana da tarihin karabkiyar 'yan Tauri masu ji da wauta cikin haɗarin Tauri.

Ab bak kaima Sakkwato gaba
Ba a zuwa hwaɗa Jabanda
Kowacce za shi kaa a hana shi
Ɗan nema kubash shi a horai

Cikon wannan waƙar yana a shafin rataye. A ƙumshiyar wannan waƙar an kawo irin hwaɗan da ya hwaru tsakanin 'yan Taurin Jabanda da wasu 'Yan Taurin da suke wani gari kamar 'Yn Jangerawa da Barkezawa a 'Yan Kaurad Dawa (Baicen Dauran).

**Jagora:** Daw wanga shingi na gabas
Hak kai wanga shingin yamma
Yaro in kagga rijiya ga baya yan Jabanda na yasa ta
Ko tsayin wata
Ko shan doguwa
Kun san shan doguwa da takobi?
Yan yara saran ƙwanda

In kagga rijiya wato rami ga bayan wani ɗan Tauri to Ɗan Taurin 'Yan Janbanda ne aka yi karabkiya da shi yay yi ma wannan mai rami rauni. Haka nan in an alama ga goshi kamar tsayuwar wata, to saran da 'Yan Janbanda na ya yi ma wani ga goshi. Idan aka ga shan doguwa wato hannu ya birkice ba aiki.

**Kammalawa**

Wannan tsakure kan Kassu Zurmi ya nuna abubuwa da dama kamar haka: Akwai waƙoƙin Kassu da yawa da ke buƙatar a tonon su a shifce su, a yi nazarin ƙumshiyarsu. Waƙoƙin kasuu suna ilmantarwa kan zamantakewa da ilmin walwalar harshen na yanki da rukuni. Kassu dai malamin waƙa ne ba maroƙi ba.

**Manazarta**

Rataye A Waƙar Kassu Zurmi ta Noma

**Jagora:**
Ya wuce maraɗa ɗan Sani
Na Bawa sannu da gyaran gona

**Y/Amshi :**
Ya wuce maraɗa ɗan Sani na Bawa,
Kwazo a barma noma

**Jagora /Y/Amshi :**
Ya wuce maraɗa ɗan Sani
Na Bawa Kwazo a barma noma

**Jagora :**
Ya wuce maƙiya ɗan Sani
Na Bawa Kwazo a barma noma

**Y/Amshi :**
Ya wuce maƙiya ɗan Sani
Na Bawa Kwazo a barma noma

**Jagora:**

Na mai Kiɗi sama gonak ka taki

**Jagora /Y/Amshi :**

Ba ɓanna ba ne
Hakanan yai daidai
Ya wuce maraɗa ɗansani
Na Bawa Kwazo a barma noma

**Jagora:**

Mui noma yan arewa mu baw wargi
Babu abin kashin garali sai noma

**Jagora /Y/Amshi :**

Babu abin kashin garali sai noma
Ya wuce maƙiya ɗansani
Na Bawa Kwazo a barma noma.

**Jagora:**

Kowa an nan arewa ɗan noma ne
Baya kau rena noma

**Y/Amshi :**

In bai yada yi ba ubanai yayi
Ya wuce maraɗa ɗansani
Na Bawa Kwazo a barma noma

**Jagora:**

Aa ɗan nadamu Uban Maigayya

**Jagora /Y/Amshi :**

Ya hana mu sayen tiyoyi
Ya wuce maraɗa ɗansani
Na Bawa Kwazo a barma noma

**Jagora:**

Kowai ma Kwazo waƙan noma
Baya yinta kaman ni
Don bai san Mayaƙi da Mani ba
Bare Na Tsohe da Amadu
Bai san Burtu bai san Sallau dogo ba

**Y/Amshi :**

Bai san Burtu bai san Sallau dogo ba
Ya wuce maraɗa ɗansani
Na Bawa Kwazo a barma noma.

Rataye B **Waƙar Ɗan Tauri Labbo Na Amadu Jabanda.**
**Mawaƙi :** Abubakar Kassu Zurmi.

**Jagora:** Gagarau na Mahamman
To,
Na Amadu Labbo mahaukata na Magaji
Ab bak kaima Sakkwato gaba
Ba a zuwa hwaɗa Jabanda
Kowacce za shi kaa a hana shi
Ɗan nema kubash shi a horai

**Jagora:** Na hwaɗa maku Jabanda ɗan daji ce
Amma hwa taci birane
Ba dai wagga yar shiya ba
Sai Jangeru tayo gayya
Jangerawa iyalin Kumba
Kila a tarbi Shanun Gandau
Masu kiyon mutun da takobi

**Jagora:** Ban dai hana yaro hawan kuka ba
Na Amadu amma hwa ya ɓantale takalmi
Hayaƙi tuƙatau
Cilas ku ka hidda na kogo
Jabanda hurunhurma maganin masukaya
Kiris ɓata kayan Jakki
Na Amadu ruwan dare ɓata kayan baƙo ya ɗora hwaɗi don ba gari nai ne ba
Na Magaji ruwan zahi maganin mai zwari
Ko dai an gunɗe ku ba a haɗe ku

**Jagora:** Banawa kun ji kiɗin Maraɗi ta Jatau
Ina da mai awon Tauri nai
Sun yi hwaɗa da yan Jabanda
Amma naku irin hali aka tsoro
Koway yi shi bai ciwo riba ba

**Jagora:** Ga hwaru can na Magaji bani hwaɗan su
Ban dai hana yaro hawan kuka ba
Amma hwa ya ɓantale takalmi
Ummmm!

**Jagora:** Kuru abun kiɗin yan anna
Cida a wa Rundawa
Dangwala a kiɗa ma anna bori
Jauje kau a wa matsurata
Kun ji irin kiɗin matsurata
Kun bani masu yankan walki
Yan Jabanda na dajinga

**Jagora:** Tsaka mai wuyas sani na Magaji
Na Amadu kahiri hwasa gayya
Ban dai bakku gudun maza daji ba

**Jagora:** Daw wanga shingi na gabas
Hak kai wanga shingin yamma
Yaro in kagga rijiya ga baya yan Jabanda nay yasa ta
Ko tsayin wata
Ko shan doguwa
Kun san shan doguwa da takobi?
Yan yara saran ƙwanda

Hannu ya birkice ba aiki

**Jagora:** Su ba Allah ba suna musakkan kansu
Tsayin wata kau saran goshi irin na Nagunda
Su nah hwaskace mai goshi
Rijiya ga baya kau saran nan na Annan Dayau
Yan Jabanda nas sare shi
Sun hwaskace mai allo
Na Amadu ya ban bak ka gudun maza daji ba

**Jagora:** To da ina zani kamo zane?
Kamo dag gabas Rukudawa
Yaƙi yaci yan Rukudawa
Aikau kwance
Sani kwance
Suri kwance
Bobo kwance
Inga nig ga an halbe shi

**Jagora:** Ina yan waɗan Kaurad dawa?
Nan wani yash shekara bai yi ko kuyya ba
Amma dai danginshi sun mai kara
Sun ɗan riƙo mai turbe
Shi kau yayi mata reno
Ya hwaɗa ma yan Jabanda

**Jagora:** Ina Gadaje na babbar unguwa?
Shi ma Gado kwance nii iske shi
Dangi na gadon ɗauka tai Karnai sun sha jini sun ƙoshi
Ya hwaɗa ma yan Jabanda

**Jagora:** Na Amadu sai dubu ta taru
Nagari kataɓurka ya warɗaɗaɗa
Godiya madalla Muhammadu Kassu ya gode ma
Allah dai ya hi ni yabawa
Kai ma Duna na gode ma

**Jagora:** Waƙat ta Labbo na Gandau
In nai gangara ko sabka
Ciki ai ba ɗumi nika so ba
Ɗumi guda nika so
Sai mai ce mani Kassu
ya ka ka ansa
Kawo anshi bata kashe ni
Da yanzu kun mance ni

**Jagora:** Na Amadu Labbo mahaukata na Magaji
Na Amadu sai dubu ta taru

Sai dubu ta taru

**Jagora:** Ina Gado rana jikan Kolo?
Shima kwance ni iske shi
Danginai na gadon ɗaukatai
Yan Jabanda sun ɓata shi

**Jagora:** Ina Sanda na Samu na Modomawa?
Su sun ka mayad dashi ɗan garki
Yak koma biyah hillani
Yacce ai ni yanzu Kassu na bah hauka
Ya koma ma garkancinai
Ihhh!

**Jagora:** Ina Wakkala kuku annen Banga?
Shima kwance ni iske shi
Dangi na gadon ɗaukatai Karnai sun sha jini sun ƙoshi
Ya hwaɗa ma yan Jabanda

**Jagora:** Ina Malan Irbo Madambaji?
Ance baya huduwa
Yan kara tcwahi sun huda
Su nah hwaskace mai goshi
Ihhhhhh!

**Jagora:** Gagarau na Muhammadu Labbo maci maza na Magaji
Na Amadu kahiri hwasa gayya
Ina ɗan sandab bakin gulbi?
Shima kwance nii iske shi
Yan Jabanda sun ɓata shi
Danginai na gadon ɗaukatai Karnai sun sha jini sun ƙoshi

**Jagora:** Sababilwa na Gidangoga
Hwarce goma ag ga mutun na hannuwa
Amma nashi bakwainai
Sauran yan Jabanda sun ɗebe su

**Jagora:** Jabanda ɗan daji ta
Amma hwa ta ci birane
Na Amadu sai dubu ta taru
Sai dubu ta taru
Na Amadu sai dubu ta taru

**Jagora:** Attanin, talata, narba an kayi alhamis, aljimma
Rannan ƙarhi tay yo gayya
Ina cikin Jabanda
Haa!

**Jagora:** Naw wuce da kalangai
Ɗauki sai taɗ ɗaukan
Ka gane mu Modomawa
Hag gabanin hantci
Rana cika tcaka sosai Ancana na cikin ban tausai
Danginai na gadon ɗaukatai
Karnai sun sha jini sun ƙoshi
Ya hwaɗa ma yan Jabanda
Na Amadu kahiri hwasa gayya
Tankwahau na Muhammadu Labbo ban bakku gudun maza daji ba

**Jagora:** Ku sha malammai daji kada a koma abutta
Ba sani ba sabo
Kowash sha wuya way aikai?

**Jagora:** Taro daurin na ɓaci Barkezawa
Labo amma yanzu na zazzaɓe
Yau dai ina da masoya
Kai dai Baura na ɗebe ka
Ba'a sa hakimmai
Sarkin hwawa na ɗebe ku
Bangaru ɗakin kara
Ban sa Ɗangaladima ba
Sani na Maikano na nan
Ko can ba dasu aka yi ba
Kuma nace ku hidda Dawaiya

**Jagora:** Amma sauran gari ku taɗe man
Yan Barkeji yan durin uwa
Yan tcelan uwam matcurata
Dauri muna biɗas su da daɗi
Labbo suna biɗam mu da ɓanna
Wai su zasu kai don tsoro
Basu san don zama ya yi kyau ba
Bari to ko mi ka bunzuma bunzum
Don dai Kassu ba ƙirau ba yankau
Mutun ya san ina da mazaizai
In ya ɗan zunguran su kashe shi

**Jagora:** Tankwahau na Muhammadu Labbo mahaukata na Magaji
Na Amadu sai dubu ta taru
Ga hwaru can na Magaji
Bani hwaɗan ku
Shanun Gandau masu kiyon mutun da takobi
Ah! Ihin!

**Jagora:** Suna ta yankan ƙamna
Sai sun yi hwaɗa da yan Jabanda

Basu san dai rubabbi ne ba

**Jagora:** Labo yace ina Katakare yayyi da Garugaru da Gandau?
In hwaɗa yas samu da Barkezawa don Allah abash shi da Sharu
A ƙyale Bala da Ɗan mai dabge
Anne kau abash shi da Dodo

**Jagora:** Nicce nima ina tamaku
Don in an ka game kubanni da Roƙo
Kai Ɗanwawu kai ab babba
Kai kau tarbe Isan Audi

**Jagora:** Muna cikin maganag ga
Sai gasu rimis rimis da kalangu
Dauran Kassuwa ta taru
An ratso cikin Jabanda
Sharu ya na ta ɓacin Gandau
Shi kau Roƙo yana ta basu kalangu

**Jagora:** To bahago ne
Sai nit tashi nit tarbe shi
Nicce to kabam matsalan nan
Mu aka lalabe da ƙahwahu
Sai an kai ka Sakkwato ɗamre
Yacce raba ni
In an kaini kak kas sa ni?
Nicce gaskiya mugunyam magana
Ga hilin nan

**Jagora:** Yat tahi Kassuwa da kalangu
Shi na ta basu Kiɗi
Shi kau Sharu na tozaya
Yana ta busag gyare Sharu yana ta ɓacin Gandau
Kassuwa ta taru ta Dauran
Hay yaz zungurai da Takobi
Ashe wai don suyi Kassuwa a raba su

**Jagora:** Kuraƙ ƙuda mai ladda
Gwabrau ba sallah daga zanne na Garba
Dogon marke ɗan bazori
A hau ku a tcere yaƙi sabka
Sabka sai gobe ga Allah
Gajimari babban dodo
Ko ka hwaɗi kahi mai ɗan ƙarhi
Na Garba Gandau na dariya shi ka ɓanna

**Jagora:** Sun ka dai ƙyale shi
Kassu ai wannan yar tcelen shegantakab banza da yohi

Ai ƙauyanci na ba hwaɗa ba
Kai!

**Jagora:** Kassuwa tana watcewa
Yan Jabanda sun tahiyyasu
Duniya da gami Dauran
Ashe yan Barkeji sun kahirce?
Ai sun dami yan Jabanda
Has sun hana su cin Kassuwa
Kun gane su can sun kore su

**Jagora:** Wawa bai san nuhwad da akai ba
Shi kau Sharu yaga yayo kora
Wai ya watce yan Jabanda
Ya hana Kassuwa taci sosai
Shi bai san nuhwad da sukai ba

**Jagora:** Barkezawa kowa yas sawo rogonai yash shaƙikke birgamanai
An taho Baicen Dauran
An sha ruwa an ƙoshi
An takikke
Daɗa hwaɗi banza hwaɗi yohi
Haa!

**Jagora:** Sai Bala ɗan Sharu yacce yau Baba kai muna daɗi
Kara da kaɓ ɓaci yan Jabanda
Ashe kocan da buladihu su ka cimmu?
Sai anne ɗan Sani yacce a'a kubam maganan nan
Ba hwa ita am mazukuta ba
Daji hwa da kunnuwa da idanu

**Jagora:** Sun kace kai ɗan bura'ubam mai tsoro
Mun sa ka cikin waɗan Jabanda
In tas samu kak ka raga muna

**Jagora:** Gaskiya mugunyam magana
Ba'a son ki sai ke tsuhwa

**Jagora:** Jabandawa Jakkuka sun ka tare su
Suna cikin sagagi
Kowane zucciya naci nai
Gandau yam miƙe
Yacce to Sharu gyara dac can
Yayyi shui kamar ruwa sun ci shi
Kamad dai ƙwai shi ɓaci ga kaza
Bai san wanda zaya hwaɗi ba

**Jagora:** Sai yaɗ ɗora ashsha Gandau

Ashsha Gandau
Hak ka ɗauki yar maganag ga?
Ai ni kasan ba nuhwata ce ba
Kocan duniya ka gama mu

**Jagora:** Yacce kai ɗan duniyad durin uwa
Yau ta hwaru ta ƙaƙƙare
Kahin a ƙara jimawa
Sai ga Sharu an kilme shi
Ga Bala can kwance
Anne an bishi an tattake

**Jagora:** Sauran barwansu sun ka hwashikke
Ina cikin Jabanda
Sai ga Roƙo kacau - kacau da kalangu
An ka ruhe da hannun riga
Na Amadu kahiri hwasa gayya

**Jagora:** To bahago ne
Sai nig gane yar tahiyatai
Nit tashi nik kame shi
Sai yaw waiwayo zats tsoro

**Jagora:** Ashsha Roƙo ɗazun ka wuce da Kiɗi
Yau ka dawo babu kiɗi
Yacce bari
yan garinmu sun ka ɓace man

**Jagora:** Nicce a'a kai Roƙo minahiki ka hwaɗa man
Mutun yay hamsin hak kay yadda sun ka ɓace ma?
Ko guda dai bashi
Kwana kayyi sun ka tciyaye?

**Jagora:** Tankwahau na Muhammadu
Labbo maci maza sai mame na Magaji annan Gandau
Na Amadu sai dubu ta taru
Labbo ban bak ka gudun maza daji ba
Ih!

**Jagora:** Yacce babu komi Kassu
Nicce ɓanna dai ce kaga an hwara ta
Na lura dakai ido na tanƙal
Yacce to na dai ga an hwara
Amma ban ga ta ƙare ba

**Jagora:** Nicce ashsha
Roƙo da wa da wa ak kwance?
Bai koma tanka man ba

**Jagora:** Kaga an buge Gandau?
Sai yay yi man na bisashe
Yag girgiza man kainai

**Jagora:** Roƙo Katakare sun ka sabatta?
Kuma sai yag gaggaɓa man kainai

**Jagora:** Kai ko sun kashe Garugaru na Mande?
Yad dai girgiza man kainai

**Jagora:** Labbo sun ka kashe?
Kassu shin wai had da ba'a?
Kasan dub ba nasu an ka kashe ba

**Jagora:** Nicce ashsha
Dawa dawa an kwance?
Yacce to naga Anne kwance
Hak kau Bala sun sarai

**Jagora:** Nicce Uban tahiyah hwa?
Wane a Uban tahiyassu?
Nicce Sharu
Yacce ai shi sun ka hwara bugewa

**Jagora:** Na Amadu sai dubu ta taru
Labbo sai dubu ta taru
Ashe dai sai da Ɓarai yaɗ ɗaukai
Bahillacen nan
Yacce ga kashi gudaji- gudaji
Ah ah mai ƙarhi ka tutu da tsamma?
Maisonai gudaji- gudaji
Waɗɗare inji yan hillani
Sharu abinga ko rogo ne?

**Jagora:** Na Muhammadu Labbo maci maza na Magaji
Sannan nicce ashsha Roƙo ban ji daɗi ba
Kai wane ashsha Roƙo?
Ai kai Kassu kai kas sa su

**Jagora:** Nicce a'a kaji wata ƙarya
A'a Kassu kai ka gama su
Nicce a'a Roƙo kai ka gama su
Kassu kai ka gama su
Nicce a'a hwaɗi dai daidai Roƙo
Kai ka gama su

**Jagora:** Laihi dai dun na Kura ne
Amma dai banda sataw wando
Ina gida zamanina
Hah!
Aa kat tahi Kassuwa da kalangai
Wai don kaga an yo ɓanna
Hak kaka tattalin ka iza man?

**Jagora:** Gagarau na Muhammadu Labbo maci maza
Sai mame na Magaji
Na Amadu kahiri hwasa gayya

**Jagora:** Ina cikin maganag ga
An yota ta ƙaƙƙare
Gandau yacce zaburi Dodo
Hwaɗa can cikin Jabanda
In ɗan maza in macce
Ko ɗan yaye ka iske cikin Jabanda
Indai ɗan Barkeji ne a kashe shi
Yau dai babu sauran ƙamna

**Jagora:** Aa Roƙo da ɗan doronai kamar yar malhwa
Bakinai kamar yar dunga
Ashe yana saurare
Wada yaj ji yar maganag
Yat tashi yaw warɗaɗaɗa wannan ya tahi sai gida a ishe mai

**Jagora:** Sai wawa sai baƙo
Na Amadu Labbo maci maza na Magaji

**Jagora:** A gode ma Ɗan Maitoka
Ɗangandau na Garba na gode ma jikan Baraka Ɗangandau Ɗansarki

**Jagora:** Sai godiya Ɗangandau
Ni Ɗangandau baka yi man rowa ba

**Jagora:** Ɗan Mani Kassu ya gode ma
Allah dai ya hini yabawa
Baka dai yi man rowa ba
Ahaa!

**Jagora:** Ɗansani Kassu ya gode
Gado Sarkin hwada ya kyauta man
Aa yai mani ƙwazo
Gado Sarkin hwada ya kyauta man
Allah dai ya hini yabawa

**Jagora:** Tankwahau na Muhammadu Labbo maci maza

A gaida Mu'azu jikan Kwasau
Na gode Mu'azu jikan Kwasau
Ummmm!

**Jagora:** Yau da ku aka komi
Ummm!
Mu'azu na gode ma
Allah dai ya hini yabawa
Gagarau na Muhammadu Labbo maci maza
Sai mame na Magaji jikan Iro.

**Rataye na C: Waƙar Ɓarawo Garba Magamin Tandu, Kaura Namoda ta Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi.**

**Gindin Waƙa:**
Ya gagari gaba Karen Galadima na Magaji,
Garba Kura mai aci wawai.

**Jagora:**
Ya gagari gaba Karen Galadima na Magaji.

**Jagora:**
Annan Sada Magaji,
Dangizgo na Ɗangido barkak ka da gaba.

**Jagora:**
Kassu na tcere ma Maroƙa,
Kowana ne na kandami kainai,
Na tcere ma Maroƙi.

**Jagora:**
Zani hwaɗa maku abinda nit tcere ma Maroƙa.

**Jagora:**
Kowa nat tahi roƙo,
Sai ya tambaya ga mai samu shi ka jiɗa,
Ni kau in na zo ga wanda ba samun nika shiɗa.
**Jagora:**
Mutun abinai ba ya gudu nai,
Na dai gode ma matcata.

**Rataye D: Waƙar Noma ta Ɗangaladima Wada Marakkai wadda Makaɗa Mamman Na Ta'ukka Gandasamu ya yi masa.**

**Gindin Waƙa:**
Kullun sai duhu Wada na gona duƙe,
Aiki yar riƙe zaman ba raggo ne ba.

**Jagora:**

Kullun sai duhu wada na gona duƙe,
Aiki yar riƙe zaman ba raggo ne ba.

**Y/Amshi:**
Kullun sai duhu Wada na  gona duƙe,
Aiki yar riƙe zaman ba raggo ne ba.

**agora:**
Alhaji nahi son ka waye man huskak ka,
Ba kai  zaniwa ba dangi na nir roƙa.

**Y/Amshi:**
Kullun sai duhu Wada na gona duƙe,
Aiki yar riƙe zaman ba raggo ne ba.

**Jagora:**
Kasan ɓace ɓace ai ba tauri ne ba,
Ni Mamman Kiɗi da waƙa su nig gada,
Alhaji dum mai hwaɗa dani bai san kunya,
Dum mai tauri ƙasag ga munas san tushenai.

**Y/Amshi:**
Don haka dum mai zuwa hwarauta yasan Nomau,
Kuma dum mai Kiɗi da waƙa ƙasag yasan Kassu.

**Rataye E: Asalin Makaɗa Kassu Zurmi daga bakinsa. Waƙar Ɗan Tauri Suleimanu Sabon Birnin Gobir.**

**Gindin Waƙa:**
Don hwaɗa aka tsoron zuwa gidan Jangwarzo,
Suleimanu ɗan maƙi gudu manzo guba.

**Jagora:**
Rad da Allah yay yoni,
Kassu rad da maisama yay yoni,
Ka ganan nan ban zo Kiɗi ba Sabon Birni,
Sai da Ummaru yay kiranmu Sabon Birni,
Sanda jikan Shawai,
Ummaru jikan Shawai: zuriyag gidan Jari Kada.

**Jagora:**
Sai da Ummaru yay kiranmu Sarki niz zo,
Amma in bancin rashin sani,
Ba baƙo ba ne gid nid dawo: gida Kurawa,
Don hwaɗa aka tsoron zuwa gidan Jangwarzo.